Wani irin Damm ƙirjin sa ya buga masa kamin daga bisani yace " Okay Kai mawa Momy Wayar muyi magana . Hasbunallah ta furta da karfi tare da sakin wayar a ƙasa ,jin Muryar Omar Farouk . When ? Tayaya ya Samu number na? Na shiga Uku .! Kasa ɗaukar Wayar tayi don anan wurin ta bar shi a ƙasa . Komawa tayi tana hayewa gadon ta , tare da jan bedsheet tana rufe kan ta , a wannan rana littafin da bata karanta shi ba kenan , duk da an inda take so a zo ,amma hakan nan ta haƙura bata karanta shi ba .

**

One class". Shine Kalmar da Ummu tayi a daidai lokacin da daliban suka kacame da surutu , gank ɗin su Beenerfa ne suka kece da dariya yayin da dayan su ke cewa " Me aikin Dafa Abinci fa tana magana , tace ayi shiru . Tsitt ki kaji Sauran Ɗaliban sunyi , Yayin da Anam da Nana miƙewa suna kallon Zee tare da cewa " wannan wani irin iskanci ne Zeee kike yi? . Ai gaskiya ce ba mai aikatau bane ita?. Murmushi Beenerfa tayi kamin tace ' ato idan karya akayi mata ai ta Muusa .  Wasu irin zafafan Hawaye ne suka fara bin kuncin Ummu , a hankali ta fara goge Hawayen nata , kamin Anam ta Yi tsalle tana cafkar Wuyar Beenerfa ji kake tass³ har sau uku tana wanke fuskar Beenerfa da mari ,yayin da Nana ita kuma ta kama Zee Suna fara kokawa . Meke Faruwa ne anan Class ɗin ?? Anam.! Suka ji Muryar Auntyn su wanda yasa su duka

dakatawa . Omar Farouk ne tare da Malaman yazo tafiya da Ummu da Beenerfa . Tsayawa yayi yana kallon su su duka , yayin Da Ummu tayi saurin saka hannun ta tana goge hawayen idanun ta . Good morning Uncle ". Ɗaliban suka yi maganan tare da miƙewa suna gaisar da Farouk , wanda kallo ɗaya yayi mawa Ummu ya kauda kai yana kallon Beenerfa da Fuskar ta duk yayi shatin mari . Antyn nasu ce tace Beenerfa da Ummu su taho ana Son ganin su a PC Office . Jakukunan su suka ɗauka , wanda suna fitowa Suka nufi moton Da Farouk ya shiga , Beenerfa ne ta fara shiga kamin Ummu ta shige gidan baya kaman kullum ,ita kuma ta zauna gyefen Farouk . Ya Farouk Walcome Back". Murmushi Yayi yana kallon Beenerfa tare da cewa ' wa ya buge ki?.

Ƙwallah ne ya ciko idanun ta ,kamin tace ' Kawai saboda nace " Wannan yarinyar tana aikatau a gidan mu Shine Ƙawar ta Anam ta mare Ni . Shiru yayi yana cigaba da driving tare da ficewa farfajiyar makarantar . "me yasa kika ce haka?."

Yayi maganan yana kallon Beenerfa , kamin cike da rashin nadama tace " Saboda Yah Farouk tana Soyayya da Yah Nurein , kuma bana Son ganin hakan . Nurein..!

Ya maimaita maganan kamin suga ya ja burki y tsaya . A hankali ya bude murfin moton sa yana ficewa tare da shiga gidan bayan inda Ummu ke zaune . Kallon ta yayi fuska babu alamun wasa kamin yace " Faɗa mun yana da kyau matar Aure tana rinƙa kula wasu mazan har su rinka soyayya ???.

Ɗago da idanun ta da suka ƙara girma na tsaban kuka tayi kamin ta girgiza masa kai alamun a'a . Keee yi mun magana da bakinki Are You deep??? Yayi maganan a tsawa ce . Cikin sauri Hawaye na cigaba da wanke Fuskar ta tace " A'a . To me yasa ke kike yi??.

Ya Farouk Saboda ita ba matar Aure bace ba. Beener ta amshi maganan tana kallon sa . Kamin ta cigaba da cewa " Kawai kayi mata warning ta kiyaye Familyn mu ,mu ba sa'oin talakawa bane ba eheee.! Waya faɗa miki ita ba matar Aure bace ba? Tana Da Aure.! Saurin kallon Sa Ummu tayi kamin cikin kuka tace " Wallahi Ni bana da Aure. Yi mun shiru ko yanzu na murje wannan ɗan mitsilun bakin naki da har yasan yace " I miss You...Yau yanzu zan koma dake garin ku ,ki tambayi Mahaifin ki , Shin kina da Aure na akan ki ko babu , Daga nan sai na dawo dake nan .!

Buɗe baki Ummu tayi cike da tsoro da tashin hankali ,kamin cikin wani irin hautsinanniyar Murya tace " A'a Wallahi bana Son ka ,bana Son ka , Abba bai mun aure da kai ba ,dauko Ni kayi ... Ke Ni mijin ki ne , tun kan kizo gidan Momy na sai da na tabbatar na mallakar kin zama tawa ,ta har Abada ,kula wasu mazan zunubi kike ai kawa babba ki sani daga yau....Luuuuuu Yaga tayi tari na ƙwace mata , hannun ta tasa tana dafe ƙirjin ta ,tare da faɗin Zafi wayyo Umma na... idanun ta yaga sun rufe yayin ......!

Kar ku manta kuyi mana Subscribe a YouTube channel ɗin mu mai suna MAMAN TEDDY HAUSA NOVELS AUDIO mun gode .!

https://www.youtube.com/@mamanteddy4123.!https://www.youtube.com/@mamanteddy4123 Subscribe our new YouTube channel pls @ MAMAN TEDDY HAUSA NOVELS AUDIO

DOMUN SAMUN LITTAFAN MMN TEDDY NA SAURARE DA ZARAR MUN ƊAURA MAZA KU YI MANA SUBSCRIBE KAR KU MANTA DA DANNA MANA LIKE MUN GODE.... https://www.youtube.com/@mamanteddy4123

R

" Hannun ta tasa tana toshe bakin ta da take jin Wani Abu na biyo mata bayan tarin nata . Idanun ta ne suka ƙaƙƙafe dai dai lokacin da Farouk ke riƙo ta yana mannata da jikin sa ...Ummu .! Kee Buɗe idanun ki .. Ummu.!!! Ya kuma kirar sunan ta a karo na biyu. Ya Farouk Jini ,Jini ya Farouk duba hannun ta kaga Ni ... Hankalin sa a tashe ya maida idanun sa kan Hannun ta , wanda nan take yaga jini duk da ba yawa ne dashi ba ,amma dagani kasan tarin da tayi ne ya fito daga Bakin ta ...Meke damun ta ne? . Tambayar da yake mawa kan sa kenan ,kamin cikin sauri yace " Beener maza yi driving ki kaimu Asibiti . Ya Farouk Mutuwa ne tayi? Ya Farouk Wallahi ina tsoro . Cikin wani irin hautsinanniyar Murya cike da doka mata tsawa yace " Cewa nayi ki koma can ki kaimu asibitin dake kusa...bana ganin gabana ba zan iya driving ba a yanzu . Jikin Beenerfa na Rawa ta fito tana nufar mazaunin Driver kamin ta shiga tana ma moton key ,cikin wani irin gudu ta ke driving din tare da nufar wani asibiti dake kusa dasu .

***

Zaune Mom Zeenatu take familyn Ɗan Shuwa duka , ciki harda Alh Ahmad Shuwa , Daddy Mom Salma duka iyayen zaune suke , idanun Mom Zeena y karkaɗa yayi jajir ,hannun tasa tana goge Ƙwallahn dake sauka mata da hankie . Domun a yanzu Mom Salma ta fayyace masu duk wani Abu dake faruwa tsakanin Ummu da Beenerfa ,daku ma Abun da Malam Kadarko ya aikata masu ,wato mahaifin Beener . Momy...!! Momyyyy tun daga Falon farko Take ƙwala kirar Sunan Momy , Wanda jin haka yasa Mom Salma Saurin miƙewa tana faɗin " My baby . Da gudu Beenerfa ta ƙariko tana faɗawa jikin Momy tare da rushewa da kuka tana faɗin " Momy Yah Farouk ya sa Ummu a tension , Tana Aman Jini ... Innalilahi wa'inna ilaihir rajiun . Duka suka furta tare da miƙewa tsaye. Me ya samu Ummun? Me Farouk ɗin yayi mata?. Daddy Yayi maganan yana kallon Beenerfa ,wanda cikin Muryar shashsheƙa ta fara cewa " Wai ce mata yayi shi ne mijin ta , Bai kawo ta nan ba sai da mahaifin ta ya daura masu aure ,don haka kula Nurein da take yi Zunubi ne . Cike da tashin hankali Mom Zeena ta riƙe Hannun Beenerfa tare da rungume ta jikin ta tana shafa kan ta , Is okay my baby , ƙwantar da hankalin ki ,ki faɗa mana yanzu Farouk ɗin yana ina ne?. Nurein ne ya tsaya turussss yana kallon su duka ,don shigowar shi Falon dai dai Beenerfa na faɗa masu yanda Sukayi tsakanin Farouk da Ummu .

Juyawa Mom Zeena tayi cikin Sauri tare da cewa " Ku mu tafi muga halin da Ummun ke ciki a

yanzu.  Hankulan su duka a tashe suka rumfato tare da nufar farfajiyar gidan ...Nurein ne ya ja moton tare da ficewa daga Harabar gidan cikin wani irin matsanancin gudu ..."

Zaune Farouk yake a gaban Doctor da take masa bayani akan ciwon Ummun yayi da cikin tsananin damuwa ya kalli Likitan yana cewa ' Kina nufin Zuciyar Ummu ... Innalilahi wa'inna ilaihir rajiun Me ya same ta? Ciwon Zuciya ne da ita ?. Furucin da Mom Salma tayi kenan Ƙwallahn da ta dade tana dannewa suka fara kwaranya mata . Miƙewa tsaye Farouk yayi ,don baiji Shigowan su Office din ba ,sai da wannan maganan nata da yaji kamar saukar Aradu . No Mom ba wani .....Kai Farouk yi mun shiru , mugu makiriiii , Duk kai ka jawo wannan Abun ,a yau Ummu ta mutu wallahi kana da kamasho akan mutuwar ta... Mom Zeena tayi magana tare da ƙarikowa izuwa gaban Farouk da yayi shiru , ko ba'a faɗa maka kallo ɗaya zaka masa ka gane yana cikin tashin hankali . Sumar jikin sa duk sun mimmiƙe . Kasan ka Auri Ummu shine zaka kawo ta aikatau ? Har ka nuna halin ko in kula da ita? Gaskiya Omar zuciyar ka babu Imani sam...Ɗago da Idanun sa yayi wanda suka kada suka yi ja Kana yace "  I'm sorry Mom". Wani irin mari ta ɗauke shi dashi Tassssss. Kamin a zafafe Ta juya tana cewa " Sai ka Rabu da Ummu , Ba zaka Zauna da ita ba ka ƙarika kashe ta . Nurein shi ya cancanta ba kai ba. Ganin Wannan masifa irin na Hajiya Zeenatu yasa Momy Saurin isa inda Omar yake tana sa Hannun tare da rungume sa tana cewa " Hajiya Zeena mubi komai a hankali ba laifin Ɗana bane ba.!

Tsayawa Mom Zeena tayi tana huci kamin Daddy suce , Duƙa mu natsu yanzu ina ita Yarinyar take ? Kuma sannan ya pacentage Ɗin Ciwon nata yake ne?. Hummmm numfawa Doctor tayi kamin tace " Alhmdllh Sir ,yanzu ma Yarinyar a ko wani lokaci zata iya farfadowa ,kuma idan muka ɗaurata akan magani zata iya rabuwa da wannan ciwon Inshaallh . Amma don ALLAH a rinƙa kiyaye mawa Abun da zai tada mata da hankali ". Juyawa Momy tayi cikin Sauri tana cewa " Ina Nurein?.  Jin haka yasa dukan su juyawa amma babu Nurein a inda suke ... Saurin fita suka yi ba tare da sun tsaya bi ta kan Likitan ba ....Farouk ne ya nufi da su inda Ɗakin Da Ummu take , shugan su ke da Wuya Suka cidda Nurein gurfane gwiwowin sa ƙasa a gaban gadon Ummu yana riƙe da hannun ta ,idanun sa ya tsira mata , zafafan Hawaye na bin kuncin sa...Mom Zeena ce zuciyar ta karaya sai hawaye sharrrrrr....!https://www.youtube.com/@mamanteddy4123 Subscribe our new YouTube channel pls @ MAMAN TEDDY HAUSA NOVELS AUDIO

DOMUN SAMUN LITTAFAN MMN TEDDY NA SAURARE DA ZARAR MUN ƊAURA MAZA KU YI MANA SUBSCRIBE KAR KU MANTA DA DANNA MANA LIKE MUN GODE.... https://www.youtube.com/@mamanteddy4123

S

Tsayawa Farouk yayi yakasa motsa ko ɗan yatsa ,duk da zuciyar sa na masa zafin Taɓa Hannun Ummu da Nurein yayi , A hankali Ummu ta fara motsa idanun ta ,tare da Ware su a saman Fuskar Nurein wanda bai san ma ta farka ba . Jan numfashi tayi tana saukewa tare da motsa bakin ta tana faɗin " Yah Nurein ."

Ɗago da idanun sa yayi wanda suka kaɗa sukayi jah , Rashin Son yagan ta cikin tashin Hankali yasa shi Sakin Murmushi yana shafa gyefen fuskar ta ,tare da cewa " Ya jikin naki yanzu? Kina jin lafiya Sosai Ummu?. Ɗan murmusawa tayi tana gyaɗa masa kai tare da cewa " Ya Nurein ina Beenerfa?. Saurin juyowa Beenerfa tayi a hankali ta fara takawa tamkar Wanda ƙwanya ya fashe mata a ciki tana isa bakin gadon da Ummu take ta tsaya ....Ɗago ido Ummu tayi tana kallon Beenerfa, kamin tayi mata magana ne Beenerfa ta ce" Ya jikin naki Ummu? Yah Farouk.....Maganan nata ne ya ɗauke sakamakon zuwa Wasu zafafan  hawaye da yazo mata . I'm very sorry for what I did . Kiyi haƙuri Ummu ....Momy Ki ba Ummu haƙuri Akan Abun da nayi mata , Ba wai bana Son ta bane ba ,a'a Haushin Fina ne da tayi kokari a class ta Zo first position ,Ni kuma second ,wannan dalilin yasa na ji bana Son ta ,ba wai bana Son ta har cikin zuciya ta ba ne ba , a'a Momy Ina Son ta , Yanzu gashi akan magana ta yana neman tarwatsa zuciyar ta , Ni ce silar faruwan komai ...Saurin isa inda Beenerfa take Mom Salma tayi tana rungume ta ,tare da shafa bayan ta tana rarrashin ta a hankali . Ɗago da Fuskar ta Beenerfa tayi a hankali Ta furta" Momy Kiyi haƙuri ina neman kashe maki gudan jinin ki yar cikin wacce kikayi naƙuda kika haifa."  Idanun Mom Salma ne yayo Waje firgici ne ya ɗarsu mata ,ba ita kaɗai ba har Nurein da Farouk da basu san komai ba , Farouk ya san Beenerfa ba yar Momy bace ,amma kuma bai san Cewar Ummu itace yar nata ba . Mom Zeena Daddy duka hankulan su ya tashi jin wannan furucin na Beener . Ummu kuwa jin kan ta take tamkar zai tarwatse saboda tashin hankali ..Wannan wacce irin magana ce Beenerfa? Meye kike faɗi haka? Momy bata da Yar da ta wuce ki, Sai dai nasan nice silsilar duka wani matsalolin ki ,shigowa ta rayuwar ku Tamkar musiba ce . Ummu tayi maganan Hawaye na cigaba da kwaranya idanun ta . Shaƙar iska Beenerfa tayi kamin ta taka izuwa gaban Gadon Da Ummu take , a hankali ta tsuguna kaman yanda Nurein yayi kamin ta cigaba da cewa" Kece Yar Momy wacce ta haifa da cikin ta ,Ni kuma Mahaifina shi ya zalunce ke ya rabaki da jin dadin ki ,ya kuma azabtar dake ....

" Da Fari ban san komai ba , Wannan yasani nake nuna miki tsananin ƙiyayya , Momy kin san a wacce Rana ce nasan Ummu yar kuce??. Beener tayi maganan tana share Hawayen fuskar ta ,wanda yafi mata ƙuna ,zuciyar ta jin ta take tamkar zata tarwatse . Shiru Momy tayi Ta kasa cewa komai ...nan Beenerfa ta cigaba da cewa " A ranan da Daddy ya fita da Ummu yayi mata shopping duk maganganun da kuka fadi bayan tafiya na dawo kuma naji ...Tun daga Wannan Lokaci na ɗauki Aniyar ganin Cewar Ummu ta rama duka abun da nayi mata , Saboda sanina a wannan Rana Daddy ya faɗa mata cewa " Kune iyayen ta , Ni kuma iyayen ta sune nawa iyayen . Daddy Ina Son ka...! Furucin Da Beenerfa tayi kenan tana ƙare zubewa tare da zaman dirshan A wurin tana rushewa da kuka mafi ciwo . Me yasa Mahaifi na yayi mun haka?. Cikin Tsananin kuka Mom Zeena ta nufi inda Beenerfa ke zaune tana riƙe ta , yayin da kowa a wurin ke share ƙwallah . Ƙwace jikin ta tayi daga na Mom Zeena ,tana ƙara Matsawa inda Ummu take hannu Beenerfa tasa tana goge mata hawayen dake zuba mata . Baki da lafiya Ummu , ba ina baki wannan labarin don hankalin ki ya tashi bane ba ,a'a Saboda na yaba miki karamcin da kika yi mun , kina da karamci kaman Momyn ki , Ni kuma na zamana yar tijara tamkar mahaifi na , Shiyasa Nurein tun a fari yayi ruwa yayi tsaki akan cewan " Kece zaɓin sa ,ke yake So ,hummmm Abun ka ga Soyayyar jini , yaji Sonki a zuciyar sa saboda kin kasance ke ɗin jinin sa ce.

Ummu ya kamata kuyi mamakin wani Abu guda ,shine ranan dana Fara yarda mukayi break fast dake ban tashi ba ,kamar yanda na saba , ba kuyi wannan tunanin ba ?. Sunan Kin san Momy Daddy mahaifan ki ne ,baki taɓa mai damun da martani akan zagi da cin mutuncin da nake miki ba . Haka Mom Bata taɓa sauya mun ko nuna mun cewan Ni ɗin ba ɗiyar ta bace .

Katse Beenerfa Ummu tayi cikin matsanancin kuka da Muryar ta har yana ɗashewa kana tace " Waya faɗa miki cewar Ke ba yar Momy bace? Ke yar Momy ne ,kina Son Momy Ni kuma Umma na nake so ,Don ALLAH mu bar a haka ...kar Umma na itama ta shiga tension Kaman yanda muke ciki a yanzu . Hummmm Ummu ba'a Taɓa Sauya mawa Tuwo suna , a bakin Daddy naji ya faɗi wannan maganan , kuma tabbas haka yake , Momy Daddy mahaifan ki ne su suka haife ki , Haka Yaya na Da kullum nake kishin sa nake jin sa a yayana jinin jiki na Mijin ki ne Ya Farouk , ina baki hakuri don ALLAH Kuyi haƙuri ki yafe mun Ummu , Ko wa a kwai irin nasa ƙaddarar Rayuwar wannan itace nawa , wanda kika gani a yanzu itace taki . Nayi miki wannan abun ne a class nace miki cook din Gidan mu ba don komai ba ,sai don ina so naga kema kin rama cin mutuncin da na dade ina yi miki ko sau daya ne ,amma baki rama ba ... Momy kullum bata sauya ba tare muke barci ta bar ki ke ,ko kiyu ko bakiyi ba bata dubawa duka saboda taga kullum ina cikin walwala . Kuna da karamci ,nice na zama na gurɓatacc.... Farouk ne yayi Saurin sa hannun sa yana rufe bakin Beenerfa tare da ɗagota yana Rungume ta da jikin sa .... Kusan mintuna biyar  shashsheƙar kuka ke tashi a wurin ... Hannun Beenerfa ya kama suna ficewa tare . Wanda nan take Momy ta kuma fashewa da kuka ,tausayin su duka ya kamata .

Tabbas Beenerfa ta faɗi gaskiya da tace " Ummu tana da karamci , don bata taɓa sanin wai Daddy ya sanar mawa Ummu cewa sune iyayen ta ba sai a yanzu kuma a yau.  Nurein ne ya taso yana Rungume Momy tare da mata magana cikin Muryar Hankali da kuma rarrashi. Mam pls Sorry for Daddy ,nasan zakiji Daddy Bai Kyauta ba faɗa mawa Ummu da yayi ,amma itama tayi hankali da bata taɓa nuna maku komai ba ta tsaya a matsayin ta na yar aiki . Yah Farouk duka shine silsilar faruwar duka wannan abubuwa .

Sir Patient din mu Bata buƙatar abun da zai rinka tada mata da hankali fa , a ko wani lokaci zuciyar ta na iya bagawa ,wanda daga nan komai zai iya faruwa ,cewan Nurse Hajja da shigowar ta kenan . Don ALLAH Alhaji Mu rinƙa kiyaye Abun da zai daga mata hankali ,ciwon nata fa....Okay Nurse Bari mu fita . Ummu kiyi barci Kinji . Cewan Alh Ahmad Shuwa suna juyawa tare da Daddy suka bar Dakin ...Nurein ne ya tashi yana ficewa shima daga Dakin ,Mom Zeena ce ta ƙarika gaban gadon tana kamawa tare da sakin mawa Ummu murmushi na tausayawa . Ɗago da idanun ta Ummu tayi suna haɗa ido da Mom Salma tayi Saurin kau da kan ta , Don bata Son Mom ta Yi mata kallon ya da Uwa ,har a yanzu zuciyar ta na can gurin Umman ta .

Lumshe ido Ummu tayi kaman mai jin barci kamin ta Hajiya Zeenatu cike da kau da komai tace

" Hajiya Salma tana son barci ne yanzu bari na gyara mata kwanciyar ...

**
Zaune suka a Bedroom din Beenerfa yayin da Har a wannan lokacin Beener kuka ta keyi idanun ta sun gagara dakatawa da xubda hawayen.  Hannun sa Farouk yasa yana rarrashin ta tare da cewa " Baki ci abinci ba Beener ,me kike Son ci a kawo miki ?. Girgiza masa kai tayi tare da cewa " No Ya Farouk , Bana Son cin komai , Yah Farouk ina Son Momy Daddy da kai bana Son rabuwa daku ... Ƙwallahn da yayi ta ɓoyewa ne suka zubo masa ,wanda cikin sauri yasa hannun sa yana ɗauke su ... ba zamu rasa ki Beener ,kin san Yah Farouk na Son ki ko?. Gyaɗa masa kai tayi alamun Ehh.  To mu nan tare.  Motsa bakin ta tayi a hankali tare da cewa " Ina so zanyi barci yanzu . Likita yace Yau za'a sallami Ummu ta dawo gida , Kaje ka taho dasu Ni zanyi barci kamin ku dawo... Okay Yayi maganan tare da gyara mata fillo yana cewa To Oyaa Sleep" . I love you Ya Farouk . Shiru yayi kamin yayi murmushi kaman yanda suka saba yana cewa " Love You too Beener . Juyawa yayi tare da ficewa daga Ɗakin , yana ɗaukar keys din sa tare da nufar farfajiyar aje motocin gidan , Don ya koma asibiti . Tana jin motsin fitar sa ,ta mike a hankali tana zama , tagumi ta saka tana lumshe idanun ta sai kuka .

A hankali ta miƙe tana nufar Waldrob ɗin ta , trolly bag din ta ta ɗauka tana fara zuba kayan ta ciki , juyawa tayi idanun ta na sauka a bango Bedroom ɗin nata , wanda a sama hoton Daddy ne ,sai gyefe da ga tsakiya hoton Momy da Farouk ko wannensu daban daban , daga kuma ƙasa nata ne . Jan trolly din nata tayi tana isa jikin bangon , hannun ta takai a hankali tana sauko da hoton Daddy da yake cikin shigar su ta manya , Fuskar shi cikin fara'a . Kanƙame Hoton tayi tana manna shi a saman ƙirjin ta , Daddy Zan tafi , Zan yi kyewar ka.... I will miss you my Dad.  Ko mawa tayi ta aje hoton a saman sofa cushine din ta ,kamin ta kuma saka hannu tana dauko hoton Momy Salma .

Baki na ba zai taba iya furta kalon ɗin da yake miki ba Momy ,ina Son ki , A Farkon rayuwata ,farkon buɗe idanuna ke na fara gani , I love You Momy and I will Miss you mam . Zan kyewar ki , Dole na Tafi saboda Baba shine silsilar faruwar duka komai namu ... Amma Ku yafe masa . Juyawa tayi tana kallon saman gadon ta ,inda Mom kullum take kwantawa duk idan zata yi barci ta kalla , tana tuno da yanda Take shafa mata kan ta tare da sata tayi barci cikin daɗin rai tayi , sai ta kuma fashewa da kuka  i love You Momy .... Ta yi maganan tare da kai bakin ta tana Kissing Ɗin pic din Momy . A Hankali ta sauke hoton daga laɓɓan ta tana ajewa a gyefe . Yah Farouk ta furta yayin da idanun ta ke akan Fuskar Farouk wanda yake ɗauke da faraa kaman bashi ne mai hade girar nan na sama da ƙasa ba . Ka nuna mun So irin na yaya da kanwa , Ka goya Ni a bayan ka babu adadi ,ka sakani dariya a lokacin dane cikin kunci ...I really Love you ya Farouk ... Kissing Ɗin Hoton shi tayi tare da ajewa kana ta dauki Hoton ta tana kallo , a hankali ta furta " Beenerfa taho ki koma wurin naki iyayen na asali. Juyawa Tayi tana saka hoton ta a cikin trolly bag din tare da ɗaukar mayafin ta tana saka kafa tare da kallon dakin nata . Daga hannun ta tayi cikin kuka tana cewa " Mom ,dad Farouk byeeeeeeeeeee.!

Juyawa tayi tana share Hawayen ta tare da barin Falon kasa tana ficewa daga farfajiyar gidan . Kai tsaye moto park ta nufa inda ta shiga buss da zai kaita garin Gombe , don tun a ranan da taji maganan Daddy na ita ba yar su bace ta yi bincike akan nata iyayen ta kuma san inda suke Rayuwa . A moton haya duk ta jigata ƙwarai don bata saba wannan wahalar ba ,ammma kuma babu yanda zata yi kamin su sauka ta gama ficewa hayyacin ta . A haka har Allah ya sauke su a garin Gombe .
**

Shigowa gidan sukayi Familyn duka har da Nurein mom Zeena , ko wannan su fuskar sa ɗauke da fara'a don jikin Ummu Alhmdllh.  Farouk ne ya kalli Momy tare da cewa " bari na kirawo Beenerfa yanzu . Okay idan tana barci ne kar ka taso ta . Okay momy Yayi maganan tare da hayewa saman Stairs ɗin falon . Kama hannun Ummu Mom Zeena tayi tana zaunar da ita tare da taba saman goshin ta tana cewa " Babu abun dake Mali ciwo ko??. Gyaɗa mata kai Ummu tayi don ita dai duk bata da walwala a tare da ita . Kin tabbata? Cewan Mom Salma tana kallon Fuskar Ummu wacce tayi kasa da idanun ta . Muryar Omar suka ji yana cewa " Momy na duba ban ga Beenerfa ba . Saurin ɗagowa sukayi mom na dafe kirji kamin tace " Ka duba ko ina mana.! Momy na duba babu Beener a cikin gidan nan ." Wani iri Dauke wuta Duka suka yi kamin Momy ta kalli Daddy tana faɗin sunan sa kai tsaye ,wanda tun da Su Omar suke basu taɓa ji ba , Abdullah Kaine ka gani ko?. Tayi maganan hawaye na fara sauka mata . Dafe kai Farouk yayi yayin da Nurein yace " Mom yanzu ina zata je kenan .? Tsayawa sukayi cirko cirko yayin da Ummu gaban ta ke matsanancin faduwa .

**
A gaban gidan mai adaidaita ya dauke Beenerfa yayin da ta fara sauko da trolly bag din ta , sallamar Mai adaidaita Tayi tana tsayawa ƙurrr tana kallon gidan , wanda ƙofan arziƙi babu , this is my own destination . Kalmar da tayi kenan tare da furta" Alhmdllh . Jan trolly din take Yi ,Kamin Ta fara nufo kofar gidan ne taga Auwalu ya fito yana buƙar Sigari ...Tsayawa yara da manyan layin sukayi suna kallon Beenerfa tare da tambayar wacece ita?. Auwalu ne yasha gaban ta yana cewa " Ke Nan ba inda kika zo bane ba , ko baki ga gidan ba irin naku bane ba ?.

A'a Yallaɓai nan nazo , Umma na ciki?. Wata Umman kuma wurin wa zaki zo a gidan nan ,kalle ki da kalli fatar ki , Banbancin ki da yan Nigeria.... Umma ne ta fito daga gidan nata da mayafi da'alama wani wurin zata tafi ...Kallon Auwalu tayi tana cewa " Yanzu Naira Talatin din magin miyar shine ka ɗauka ka siye Sigari ? To Umma a haƙura da girkin yau ,Ni idan ban sha sigari ba ban jin dadin Rayuwa . Ummmaaa.!

Beener ta kira sunan Umma tana tsayawa tare da bin ta da kallo . Cakk Umma ta tsaya tana yin mawa Beener ƙurrr da ido . Girgiza kai Umma tayi tana saka gyefen mayafin ta tana sharce hawayen daya zubo mata . Nasan dama wannan ranan dole wata rana zai zo . Domun duk abun dake faruwa zuwan Alh Abdullahi Shuwa naji duk abun da ya wakana da Malam Kadarko . Shigo daga ciki . Bin bayan umma Beenerfa tayi jikin ta a sanyaye babu wannan kuzarin nata . Wacece Wannan kuma Umma? A ina kuka samo mana jinin turawa?. Auwalu yayi maganan

yana cigaba da buƙar sigarin sa .

Sam umma bata basa Amsa ba , Trolly din Beenerfa ta Amsa suna shigewa daga ciki , a cikin zauren ne Beenerfa ta riƙe Umma gammm don gani take tamkar Soron zauren zai faɗo mata aka . A haka suka shiga tsakar gidan  dai dai Malam Kadarko na fitowa daga dakin sa da buta a hannun sa . Wacece Wannan ?. Kallon sa Umma tayi tana kauda kai cike da jin Zafin abubuwan da ya aikata shekaru sha bakwai baya . Abun da ka shuka ne yau ka girbo , baka gane ba ? Ai yar kace Beenerfa da ka musanya a asibiti ,yau Ummu ta koma gidan su itama kuma da kafarta ta dawo nasu gidan. Tari ne ya kwace mawa malam Kadarko kuful³ . Haushi ne ya kama Umma wannan yasa ta kama hannun Beenerfa tana cewa " Shigo daga ciki .  A bakin gadon Umma Beenerfa ta zauna tana yin shiru ,kamin ta ji Muryar Umma cikin kuka tana cewa " Ina Son Umma na ,ina Son Shalele na a yau ta bar Ni...! Malam ka cuceni kuma ka cuci kan ka. Saurin miƙewa Beenerfa tayi tana tsugunawa gaban Umma tare da rungume ta tana cewa " Umma kiyi Haƙuri komai bai Baba yayi maki ki yafe masa . Ke Kadarko baya da hali ,kalli Abun da yayi maki Wanda nasan har Abada ba kowani yaro zai yafe mawa iyayen sa da sukayi masa wannan yankar ƙaunar ba . Girgiza kai Beenerfa tayi sai hawaye sharrrrrr³ , Umma Ni na yafe mawa Baba kema ki yafe masa , koba komai shine wanda ya haife Ni ....! Shiru Umma tayi tana nazarin kalaman Beenerfa kamin ta miƙe tana ficewa daga Ɗakin tare da nufar Ɗakin Malam Kadarko wanda ya shige tun ganin Beenerfa da yayi .

***

Ɓangaren Momy da Daddy sun ɗauka Beenerfa tana gidan kaka ne ,wannan yasa Su nufar gidan ,da duk inda suke tunanin zata je amma babu ita , a ƙwana na ɗaya ne Ummu itama ta gudu ,wanda anan ne suka mai da hankalin su wurin nufo Gombe .
Da misalin hantsi wuraren ƙarfe Biyu na yammaci ne Auwalu na Zaune a a dakalin Mudi mai rake yaga fitowar Ummu daga napep . Cikin Sauri ya ƙarisa inda take ,tana kallon sa ta fashe da kuka Ya Auwalu ina Umma na?. Sakin Baki Auwalu yayi kamin yace "Ashe ke shashasha ce Allah yakaiki gaba kin huta da kangin Talauci shine kika sake dawowa cikin fitinan wannan talaucin gidan ?. To an gane ke ba yar su bace ba ,dama Baba ne yayi komai don haka yanzu shawara Ummu ki koma wurin iyayen ki masu kuɗi ,idan kin samu nasan ki da zuciyar rahama don ALLAH kar ki manta dani... Juyawa Ummu tayi tana yin gaba tare da nufar cikin gidan , kan ta tsaye ta kutsa tana kirar Sunan " Umma na.! Umma na .!!

A farfajiyar gidan ta hango su , Umma na tankaɗar Gari , Beenerfa na Wanke wanke...Miƙewa Umma tayi da Sauri , Yayin da Ummu ta nufe ta tana rungume ta jikin ta . Aje Soson Beenerfa tayi tare da nufowa inda Ummu take , A hankali tasa hannun ta tana ɓanɓare Ummu daga jikin Umma kamin tace " Nan ba gidan ku bane ,Gidan mu ne ,ki fita bana Son ƙara ganin ki a cikin gidan nan . Beener Pls Beenerfa ki Yi haƙuri , ni Umma na nake so.! Nima ita nake so.  Just Outttt...! Tayi maganan tana fizgar Ummu tare da hankaɗata nan take tayi ƙasa tana faɗi.

Can yafi dacewa dake Ummu ki tafi . Umma tayi maganan tana xubda hawaye , Saurin miƙewa Ummu tayi tana cewa "a'a Umma na ke nake So. Sallamar Momy Salma ne yasa su duka juyawa suna kallon ta . Tsayawa tayi tana bin Beenerfa da kallo wanda itama tana ganin Momyn

naya zuciyar ta ya karaya . Bin gidan da Take ciki Beenerfa a yau tayi ,kawai sai Momy ta fashe da kuka , Ware mata hannu tayi wanda da sauri Beenerfa ta faɗa jikin ta tana rungume ta....!

*Littafin THE VIRGIN MAID na kudi ne ... Regular group ₦300... VIP group₦500... Special ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko katin MTN ta wannan number 08081202932....Ina Kira ga masu ba wasu kudin littafaina suna faɗin wai Ni maman teddy na wakiltasu ,su ɗin Wai wakilai na ne , To Wallahi Ni Maman teddy ban san su ba , Kawai Scammers ne yan damfara su amsan miki kuɗin ki ,daga bisani suyi blocking naki , da yawa a rana fiye da mutane 4 biyar suna zuwa mun akan wannan matsalar sun tura mawa wasu kudaden su since masu wakilai na ne To ƘARYA ne , bana Wakilta kowa a harkar Sayar da littafaina ,Ni nake rubutawa don haka nice mai sayarwa , ga number na da kullum zaku same Ni 08081202932 ko kuma wannan numbern 09061466409 bayan Wannan nombobin ban san kowa ba , Scammers ne . Ga kuma gerangiyar littafan nawa nan a ƙasa , saboda na ƙara Wayar mawa mutane kai akan wa'annan masu damfarar yasani na saki wannan PAGE din Bonus.* *WALIJAAM, YAR WAYE , SIYASATA ,DIJAMA YAR FULANI, GIDAN ƘWARATA , KWARTON MANYA , THE SEXXYY BOSS ,MY LADY BOSS ,ZUMA DA MAƊACI , KAWALIYA ,HABIBI DA'IMAN, BINTOTO, BAFULLATANAN RUGA , SIYASATA , GIDAN KWARATA , ƘWARTAR SAMA , SADAKA YALLA , TAƁARAH , ƳAR AIKI NA GASUNAN LITTAFAINA DA YAWA A SOCIAL MEDIA ,DUKA NIKE SAYAR DA KAYA NA , BA WANDA NA TAƁA WAKILTAWA GA KUMA NUMBER NA 08081202932 BAYAN HAKA KO WAYA AMSA KUDIN KU TO DAMFARA NE ,NI BAN SAN SHI BA BAN KUMA SAN TABA, DON ALLAH ZAKU NA IYA SHARING WANNAN SAƘON DOMUN WANDA AKE DAMFARA SU FARGA SU GANI SU KUMA SANI...MUN GODE...!*https://www.youtube.com/@mamanteddy4123 Subscribe our new YouTube channel pls @ MAMAN TEDDY HAUSA NOVELS AUDIO

DOMUN SAMUN LITTAFAN MMN TEDDY NA SAURARE DA ZARAR MUN ƊAURA MAZA KU YI MANA SUBSCRIBE KAR KU MANTA DA DANNA MANA LIKE MUN GODE.... https://www.youtube.com/@mamanteddy4123

T

Rungume Juna suka yi Beenerfa da Momy ko wannen su na ƙwallah na ƙwaranya daga idanun sa, cikin Sauri Ummu ta nufi Umma tana faɗawa jikin ta ,tare da Fashewa da Kuka , dai dai su Yah Farouk Daddy ya Nurein na shigowa gidan . Ko wannan su ja yayi tsaya zuciyar su a karaye kuma cike da Tausayin junan su . Malam Kadarko ne ya tsaya jiki a sanyaye domin shima fitowar sa kenan daga Ɗakin sa . Kallon sa Hajiya Zeenatu tayi kamin cike da ɓacin Rai ta hau cewa " Yanzu me kayi kenan? Abun da ka shuka yau gashi ka girbe kayan ka , Anya Wa'annan Yaran da kayi masu yankar ƙauna zasu yafe maka kuwa?. Wallahi ka nemi gafarar su ,sannan kuma ka nemi tuba zuwa ga nahalicci ... Kallon Mom Zeena Ummu tayi idanun ta na tsaka da zubo da hawaye ta motsa bakin ta daƙyar wurin cewa " A'a Momy duk Abun da Baba na yayi ,ba kansa bane , Allah ya hukunta dama hakan zata faru , Kuma da sharrin shaiɗan kuyi haƙuri Ku yafe mawa Baba ". Kallon ta Umma tayi tana girgiza kai Ƙurum ,zuciyar ta tafi mata zafi fiye da raɗaɗin hawayen dake sauka mata . Tabbas zan yi rashi kuma zan yi kyewar Ummu

, Yarinya mai Hankali tawakalli haƙuri juriya , Amma yana iya hakanan zan baku ɗiyar ku , Daga Kuma ƙarshe Don ALLAH Hajiya Salma , Alh Abdullah Ina Mai Baku haƙuri bisa ga Abun da Malam ya aikata maku akan jinin ku . Umma ta ƙare maganan wasu irin Zafafan Ƙwallah na zubo mata . Malam Kadarko ne ya amshe maganan nata cike da matsanancin nadama da dana sani ,ga kuma kunyar Abun da ya aikata .

Kuyi haƙuri bani da baki ko wata kalmar da ta wuce mun wannan ,duk da na san da wuya ku iya yafe mun . Baba Nice Yar ka kayi mawa Hakan , kuma tsakanin Uba da Ɗa babu kalmar yafiya ,Ni yar kace kome kayi mun dai dai ne Baba . Ummu tayi maganan tana Matsawa Kusa da Malam Kadarko da idanun sa suka kaɗa sukayi jajir , Ƙwallah ne ya ciko idanun sa jin furucin Ummu akan sa . Tabbas sai a sannan ya fara jin Abun da Umma take ji na Rabuwa da Ummun ,tabbas zasu yi kyewa ƙwarai kuma sun yi rashi . Gaban sa ta tsaya tana sa hannun ta tare da goge masa ƙwallahn idanun sa kana cikin maida komai ba komai tace " Baba Meye na kuka ,ka bari don ALLAH , Idan Beenerfa kake tunani Daddy Umma na ko Momy duka Ni nasan sun yafe maka .

Gyarar Muryar Da Daddy Yayi ne yasa su ,su duka mai da hankulan su akan sa . Kamin ya ce " Ƙwarai Kuwa Ummu ,an zama Ɗaya komai ya faru na rashin jin daɗi mun yafe , Allah ya yafe mana baki Ɗaya . Amin Ya rabil Alamin , cewan Su duka kamin Momy da Umma su shige Ɗakin Umma , duka har da Hajiya Zeenatu , Farouk Nurein ,Auwalu daddyn Nurein ,Daddy Baba Kadarko a tsakar gidan suka zauna ana shimfida masu tabarma , anan suka zauna kowa nan su na ba ɗan uwan sa haƙurin Abubuwan da ya faru . Kusan ƙarfe Biyar na yammaci Daddy ƴace su fito domin su ɗauki Hanyar komawa Abuja . Gaba Ɗaya Ummu babu walwala duka a tare da ita ,duk da tana san ran dawowar Beenerfa cikin gidan , don sosai taga ta saki jikin ta tun da Momy Tazo tana jikin ta har izuwa yanzu da suka fito domin tafiya . Hannun Beenerfa Momy ta kama dana Ummu ,wanda cikin Sauri Beenerfa ta kalli Momy tana girgiza mata kai No Mom ba Zan bi KU ba , Ina so na zauna da Umma anan nima . Wani irin bugawa Ƙirjin Momy yayi wanda ya sata saurin kallon Beenerfa kamin tace mata Wani Abu ne Farouk yace " Ke Beener taho mu wuce , me zakiyi anan Ɗin ?. Taho .! Ɗago da rinannun idanun ta tayi tana kallon sa ,kamin da sauri ta nufe sa tana faɗa wa jikin sa rungume ta yayi tsam jikin sa , wannan wacce irin musiba ce? Tambayar da yake mawa kan sa kenan ? Kamin yaji Muryar ta tana cewa " Yah Farouk bye. Tana Juyawa da sauri tana shirin wuce Momy , cike da zafin nama Momy Tasa hannu tana riƙo ta . Pls Beener Kar ki son zama damu ,don a yanzu Kinji mu ba iyayen ki bane , Beener Ni Momyn Kice ba zan taɓa sauyawa daga hakan ba har abada . Wani irin huci Beenerfa ta sauke Na Wanda yayi kuka yayi har ya gode Ma Allah ,kana ta kalli Mom Salma tana cewa " I love You Momy , And I love my family , Ina Son zama da Umma na ,ba don komai ba sai don itama na saba da ita kaman yanda na saba daku , Kuma zan ji Dadi nima naga nasan Wasu dangi na ko ba duka ba , Mom Ku tafi ,ina fa anan , a duk lokacin da nake son Ganin ku zan zo.! Kar kisa Wannan a Ranki har abada bazan taɓa iya sauya ki a uwa ba , Saboda ba zan iya ba ....ta ƙare maganan tare da Fashewa da wani irin kuka mai gunji , Cike da tashin hankali Mom Salma ta sa hannun tana hugging ɗin Beener zuwa jikin ta ,kuka suke sosai

, yayin da kowa na wurin sai da ya xubda ƙwallah na tausayawa . Kusan mintuna biyu suna ƙanƙame da juna kamin Beenerfa ta ɓanɓare kan ta ,da sauri tana faɗin " Momy Bye bye , ta ƙare maganan tana barin wurin da gudu . Ummu dake tsaye ne idanun ta har basa gani saboda kuka da kumburar da suka yi , Ba tare da ta ankare da zuwan sa ba , Sai hannun ta da taji ya riƙe yana furta " Mu tafi .!

Saurin ware idanun ta tayi a saman fuskar Nurein ,kamin ta juya tana kallon Farouk wanda suna haɗa ido yayi mata wani irin kallo ko na meye bata fahimta ba . A hankali ta fara bin bayan Nurein yayin da Momy Salma cikin matsanancin damuwa ta fito gidan , Hajiya Zeenatu ita ta tsaya sallama da Umma ,itama duk taurin zuciya irin nata ta gagara ɓoye Hawayen ta . A wannan yammaci suka ɗauki Hanyar dawowa Abuja ,ko wannan su Ka kalli Fuskar sa babu walwala sam."

"Bayan Wasu watanni".

Parking moton sa yayi a Inda aka tanada na aje motocin gidan , Kana ya fito cikin zatin sa ,idanun sa na a cikin ɓakar tabarau . Ga wani Saje da ya kuma ajewa fiye dana da baya . Wani ƙyau ya ƙara na musamman . Cike da earphone ɗin Kunnen sa yaji Muryar Momy tana cewa " Welcome back my Son , Ina Under ground . Murmushi Farouk yayi kamin yace " Okay mam . Cike da takonsa na matashin Soja yake takawa cikin sassarfa yana nufar Part din Momy Salma .
Cike da matsanancin Farin ciki ya fara wuce falon gidan yayin da ma'aikatan ke gaishe sa amma da yake baya ta kansu ,mutum biyu ya kosa ya gani Ummu da Momy , don sun fi watanni Hudu basu haɗu ba , Ta dawo gidan da kwana biyu yayi tafiyar su ta sojoji sai a yau ya dawo . Yana shirin bin lifta zuwa under ground na ga mom har ta fito da Sauri tana hugging din Farouk cike da matsanancin Farin cikin ganin sa . I'm happy to see you Son . Ya hanya ? Tayi maganan tana ɗagowa daga jikin sa cike da matsanancin Farin ciki . Murmushi yayi yana faɗin " All is Well Mam , Ina Ummu take?.

Fuskar Momy ne ya sauya a lokaci guda ,idanun ta na ciko da ƙwallah , a sanyaye tace " Tana Bedroom ɗin ta . Okay Yayi maganan yana raba jikin sa dana Momy tare da Son nufar Bedroom din Ummun . Hannun sa Momy ta riƙe a hankali ta fara faɗa masa halin da suke ciki da Ummu a gidan , Sam kullum ka ganta cikin damuwa take ,taƙi sakewa dasu , Idan kaga Walwalar ta to da Nurein ne idan ya zo , ko break fast Bata Sanyi dasu , idan ko ta zauna a ɗaki ita kadai bata da aikin da ya wuce na kuka . Idan na tambayeta meke damun ta sai tace babu komai . Momy Kiyi haƙuri Kinji ? Zata dawo yanda kike so Inshaallh . Farouk don Allah kayi mun kokarin hakan , ina damuwa sosai idan na ganta a hakan . Gyaɗa kan sa yayi alamun to ,kamin ya juya yana saurin hayewa Stairs ɗin da zai kasa Bedroom din Ummu .

**

Zaune ya hangota kafafun ta na naɗe saman kujerar da take kai , hannun ta rungume da teddyn ta , Idanun ta a lumshe suke amma hawaye ke zuba mata , Sosai ta sauya tayi kyau ta ƙara murjewa fatan ta har sheƙi yake , tsayawa yayi yana kallon ta don bata san da shigowan sa ba ,alamu tayi nisa a tunanin da ta saba . Ummu.! Taji Muryar wanda bata yi expecting ba ya Kira sunan ta , cikin Sauri ta ware idanun ta tana kallon inda yake a tsaye . Murmushi ya sakin mata ,wanda tun da suke bai taɓa mata irin shi ba . Yah Farouk ka dawo?. Hummmm bai bata amsa ba sai zama da yayi kusa da ita ,yana sa hannun sa tare da zagayowa ta gyefen kafaɗan ta . Meke damunki?. Yayi mata maganan yana mata ƙurrr da ido . Saurin Girgiza masa kai tayi alamun a'a babu komai . Amma sai ya kauda kan sa kaman bai ga me tayi ba ,cewa nayi meke damunki ,buɗe baki kimun magana . Cikin Ɗan rawar murya ta ce " Babu komai . Kin tabbata?. Yayi mata maganan yana kallon ta ido cikin ido . Shiru tayi masa kamin ta kuma cewa " Eh . Murmushi yayi yana ɗan yin shiru tare da nazarin ta , hannun sa taji yasa yana ɗago Fuskar ta ,kamin tayi Aune ita dai taji ya haɗa bakin shi da nata ne yana tsotsan laɓɓan ta , wani irin abu taji yana mata yawo a ƙwanya wanda bata taɓa ji ba ...Ƙoƙarin janye kan ta take amma ina riƙon tamau yayi mata motsi ƙwaƙƙwara ta kasa . Ji tayi yana lalubar Harshen ta tare da cafkar sa yana cigaba da sha mata yana tsotsa mata tare da mannata jikin shi , nan take ta koma wata ƴar Babe da ita , gaba ɗaya ya rufe ta . Numfashin ta ne ya fara ɗaukewa na tsoro ,wanda sai a sannan ya zare harshen sa yana sauke numfashi tare da kauda kan sa tamkar bai mata komai ba . Gyefen sa ma yake kallo inda kayan tarkacen make up din ta Suke . Tsayawa tayi jikin ta ko ina rawa yake yi wanda kamin ta gama dawowa hayyacin ta ne taji ya kuma cewa" Meke Damun ki kike kuka kaɗai anan ?. Yah Farouk babu komai . Okay Yayi maganan tare da juyowa yana passing din Fuskar ta ,hannun sa taga yasa yana ɗago fuskar ta tare da shirin haɗa bakin shi da nata ,wato yayi mata irin yanda yayi mata yanzu . Ya...yah Farouk Please ,ka bari don ALLAH ...shii meke damun ki to?. Yayi maganan yana ɗaura yatsar sa a laɓɓan ta alamun tayi masa shiru sai kuma ya kuma maimaita mata tambayar? . Cikin Muryar shagwaɓa kuka na shirin ƙwace mata tace " Gida nake So naje. Ina kyewar Umma na , Beenerfa duka .

Jikin sa ne yayi sanyi ,a hankali ya sa hannun sa yana tallabo fuskar ta kamin yace " Okay zan kai ki gida ,amma sai da sharaɗi guda ,kome ne nasaki yanzu babu musu kin amince? Idan kin amince next week Zan Kai ki Gombe ,kuma ki daina noƙe mawa Momy tamkar ba Mahaifiyar ki ba ,ina so ki sake da ita tamkar yanda kika saba da Umma Kinji . Gyaɗa masa kai Ummu tayi cikin sauri ,kamin taga Ya miƙe yana cewa " Yau goyaki zanyi ,sau nawa kike Son mu zagaya Bedroom din Nan naki ?. Ware idanun ta tayi cike da mmki kamin tace " A'a . Kallon ta yayi yana jin babu daɗi ,don so yake yaga yasata nishaɗi da walwala kaman yanda Mom ke So. Wayar ta ne ya fara ringing ,Wanda cikin sauri idanun ta suka fito ganin sunan Nurein , hankalin ta ne ya fara tashi , kasan daga Wayar tayi sai kallon Farouk da take yi ,wanda shima ita yake kallo . Saurin aje Wayar tayi tana kashe ta baki daya . Har a lokacin Farouk bai ce mata komai ba yana kuma anan tsayen da yake , wannan yasa ta miƙewa a hankali idanun ta na cikowa da ƙwallah , takawa tayi tana zagayawa ta bayan sa kaman yanda yace mata , hannun ta tasa tana rungume sa tare da ƙwantar da kan ta a gadon bayan sa . Wani irin zuuu zamm zamm yaji ,wanda yasa shi Saurin lumshe idon sa yan jan ajiyar zuciya . Ƙwantawa tayi a bayan basa yayin da a hankali ya ɗan rage tsawon sa tana hayewa ya goya ta cak... Shashsheƙar kukan ta yaji amma bai dakata ba , nufar ƙofar fita yayi yana ficewa da ita zuwa love garden nasu na

gidan ,inda suka saba hutawa . Tsayawa tayi tana kallon wurin don bata taɓa sanin dashi a gidan ba".

*Littafin THE VIRGIN MAID na kudi ne Regular₦300 VIP group ₦500 SPC₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko katin MTN ta wannan Numbobi 08081202932*
Alhmdllh alah khulli haaleen.!https://www.youtube.com/@mamanteddy4123 Subscribe our new YouTube channel pls @ MAMAN TEDDY HAUSA NOVELS AUDIO

DOMUN SAMUN LITTAFAN MMN TEDDY NA SAURARE DA ZARAR MUN ƊAURA MAZA KU YI MANA SUBSCRIBE KAR KU MANTA DA DANNA MANA LIKE MUN GODE....
https://www.youtube.com/@mamanteddy4123

U

Bin wurin Ummu take da kallo cike da jin dadin ganin ta a wannan Wurin , Yah Farouk sauke Ni . Kin bar kukan ? Gyaɗa masa kai tayi cikin zazzaƙar Muryar ta tace " Eh ai dama Ni Umma nake Son Gani shiyasa nake Kuka . Hummmm numfasawa yayi tare da sunkuyawa ƙasa kaɗan yana cewa " Okay Sauka to. A hankali ta sauka tana murmushi tare da juyawa tana kallon gyefe da gyefen Wurin baki ɗaya . Tsayawa yayi cike da jin dadin ganin ta a wannan yanayin ya koma yana zama a wani rest chair dake wurin a can gyefe . Wow ,Nan Wurin yanda kasan ba A Nigeria ba ... Saurin kallon gyefen ta tayi ,nan taga babu Farouk , cikin Sauri ta juya tana shirin sa ihu don wurin babu kowa sai Muryar shi taji daga bayan ta yana cewa " Yadai Madam kuka , Bakya gajiya da yin kuka ko da yake Ni nasan shagwaɓa ne yayi maki yawa . Kallon sa tayi tana ɗan cuno masa baki kamin ta yafito sa da hannu alamun yazo . Miƙewa yayi yana Matsawa zuwa inda take tsaye . Ɗaga kan ta tayi tana kallon Fuskar sa , wanda ta tsaya iya kafaɗan sa . Kai na namun zafi ,ba zan iya dunga ɗaga kaina Sama ba Yah Farouk ka sun kuyo ƙasa mana . Kallon ƙasa ƙasa yayi mata mai nuni da fassarori da dama kamin yasa hannun sa cikin aljihun sa yana sunkuyo da kan sa ƙasa tare da ɗan rage tsawon sa . Buɗe baki tayi zata masa magana sai taga yana nufo da bakin sa zuwa lips ɗin ta . Da sauri ta kauda kai tare da kai bakin ta sai tin kunnen sa tana raɗa masa Wurin yayi mun ƙyau ya Farouk.
Gani tayi ya tsaya yana kallon ta bai ce mata komai ba sai zuba mata idanun sa da yayi baya ko ƙiftawa , hannun shi taga yasa yana ɗago da fuskar ta ,a hankali yasa Bakin sa yana tsotsan laɓɓan ta cikin salon sa zafi zafi ...Ƙoƙarin janye jikin ta take , Hawaye na ciko idanun ta , ganin tana shirin saka masa gardama yasa shi , kama mai gaba ɗaya , abun da bata taɓa jin yayi mata ba , hannun sa yasa yana kama Breast din ta wanda yasa ta ɗauke wuta jin yanda yake ligwigwitar su , A hankali ya zare bakin sa daga nata kamin yace " zaɓa ɗaya Wanne kike So? Nan ko nan ? Ya yi maganan yana Kissing ɗin saman lips din ta , sai kuma ya nuna mata nonuwan ta da hannun shi ,wato ta zaba wanne ciki take so yayi mata . Don ALLAH kayi haƙuri ,Ni baka ce mun haka zaka mun ba shi yasa na biyo ka , Wayyo....Shiiiii Kara kame bakin ta

yayi yana cewa " Okay bara nayi maki duka . Jin hannun sa tayi yana cukurkuɗar nonon ta ,wanda tuni hawaye ya fara wanke fuskar ta ,don har ga ALLAH taɓa mata nonon da yake zafi suke mata . Gashi ya riƙe ta tsam motsi ta kasa yi , tsotsan bakin ta kuwa ji take tamkar yana mata waiwayi...kusan mintuna Huɗu yana ligwigwita duk inda yaso kana ya ɗago a wahalce dagani kasan yana tsananin buƙatar ta mace tare dashi ...idanun sa sun sauya , cikin wani irin murya yace " Me kika ce? Ummu zaki bini muje Gida na yanzu? Please?? Yayi maganan bai ma san yayi ba . Fiddo da idanu tayi jikin ta na ɓari na tsoro tace" don kar kamun komai ,bazan je ba Wallahi . Ta ƙare maganan tana shirin guduwa , hannu ɗaya yasa yana riƙe ta . Kana ya kalle ta yana sakin murmushi kaman bai mata komai ba." Kallon ta yayi yana kara Murmushin nan nasa kana yace " Kema a gidan ki aƙwai irin nan Wurin ,kina So kigani? Just trust your Life , Ba Abun da....Ni ba zani ba , wallahi ba zaku haɗu kai da Ya Fahad KU kashe Ni ba ,irin yanda kukayi mawa Wancen yarinyar ta ranan nan. Kuma Ni Na faɗa mawa Momy Yah Nurein nake So ba Kai ba.

Wani irin abu yaji yazo masa wuya mai ɗacin gaske ,wanda nan take ya sake ta yana mata Wani irin kallo mai cike da tsananin ɓacin Rai da kishi . Okay kin san Waye Nurein a wuri na? Ƙanina ne Uwa ɗaya Uba ɗaya , ba kuma zai Aure ki ba na faɗa miki , Wannan maganan da kika faɗa mun duka sai kinyi dana sanin faɗar su , Abubuwa biyu kenan nake bin ki bashi , Marin da kika mun ,da kuma Wannan maganan .

Ƙirjin ta ne ya buga sam ta manta da marin da tayi masa , Muryar sa taji yana cewa " Saura idan kin shiga ciki ki faɗa masa Momy cewa nayi kissing din ki ko na taɓa maki nono , zaki faɗa?. Yayi maganan yana tambayar ta fuska babu rahama gira a haɗe .

Ja baya tayi tana gyaɗa masa kai cikin kuka tace " Wallahi sai na faɗa mawa Momy ,ta daina bari kana zowa inda nake , zan faɗa mata abun da kayi mun. Wani irin murmushi yayi kamin ya ɗaga hannun sa yana cewa " Da ƙyau , that's what I want to hear , ki faɗa mata daganan ba zaki ƙara sati guda ba a gidan nan zaki dawo gida na wato gidan mijin ki da zama . Wallahi ba zan faɗan ba...Ta ƙare maganan tana rushewa da kuka irin na tashi ga ukun nan. Kallon ta yayi yana cewa " Gyara Rigar ki mu wuce ciki , ko na gyara miki ne?. Hannun ta tasa tana saurin gyara bra din jikin ta da yayi sama dashi don ya yi abun da ransa ke so . Ji tayi ya kama hannun ta yana Wucewa da ita zuwa falon Momy . Fitowan Momy Salma daga kitchen kenan dai dai suna shigowa ,wanda cikin matsanancin Fara'a da jin dadin ganin su a tare a haka tace " Farouk kai Ummu Rest Room ta huta kamin na gama....Kamin Momy ta ƙarike Ummu ta fasa ihu har da buga ƙafa tana cewa " Wallahi ba zani dashi ba , kin san meyake mun ne? Ni bazani ba. Tana maganan ta haye sama da gudu tana barin falon cikin kuka.

Shiru Farouk yayi ,kan sa a ƙasa tun da yake bai taɓa jin kunyar wani Abu ba sai a yau ɗin nan ,ganin Momy a gaban sa . Gyarar murya Momy tayi kana tace " Je ka rarrashe ta Farouk uhmm?. Okay Yayi maganan yana bin bayan Ummu . Kallon sa Momy tayi kamin tace " Farouk matar sa ,ya kamata Daddy mu tsaida ranan tarewa a satin nan ayi a gama komai . Ta ƙare maganan tana gyara zaman ear phone din dake kunnen ta ,don tun shigowan su magana suke da Daddy ta Waya . Kar ki damu bari na dawo ,zan zaunar da Farouk ɗin muyi magana naji ."

Okay Shine kalmar da Momy tayi tana takawa tare da nufar Dirning Area .

Kama kan ta tayi da gwiwa tana kuka , wanda koda taji an murɗo Handle door din Bata ɗago ba , ƙamshin turaren sa da ta shaƙa ne yasa ta fahimtar Farouk ne ya shigo , cikin sauri ta miƙe tana rarraba lulun idanun ta...Humm zaki yi shirun ko sai na yi miki abinda bakin naki zayyi shiru don dole ?. Tsitt tayi tana daina kukan nata . Wani kallo yayi mata yana sakin murmushi mai fassarori kana yace " ina Tausaya miki Yarinya , Bakya baki da Kunya ba? Zan yi maganin ki . Yana gama faɗa mata haka ya juya tare da ficewa daga Bedroom ɗin nata .

**

A hankali suke shiga layin Ummu sai Nurein da ya kawota tun daga Abuja zuwa Gombe . Ba tare da ta tsaya ko Momy ta sani ba , duk da shi a yanda tace masa Momy tasan da tafiyar nata , bai san ba haka bane ba ,don Company n sa ta biyo sa akan ya kawota Gombe.  Yauwa Yauwa yah Nurein mun zo . murmushi yayi yana cewa " To shiga sai ki faɗa masu tare muke yanda zasu shirya kar Na shiga gidan babu excuse . Dari ya Ummu tayi kamin tace " Okay Sir . Waye Sir ɗin anan? . Juyowa tayi tana dariya tare da cewa" Haka da naji ma'aikatan ka nace maka . Kema sau ki cemun ?. Ok I'm sorry , na Manta ne My Champ. Dariya yayi itama tana dariyar ta fice daga moton tare da nufar gidan Malam Kadarko . Wani irin tasss³ take ji tun daga zaure ƙarar mari baba Wasa ba , yayin da Muryar umma ke kai kawo tana kirar sunan Auwalu ? Kana da hankali kuwa ? Me tayi maka? Auwalu zan buga maka Wannan itacen. Saurin kutsa kai Ummu tayi tare da shiga gidan . Auwalu ne taga ya kama Beenerfa yana duka da mari , yayin da Umma itama ke bugun shi da itace. Wannan yasa shi sakin Beenerfa dake ihu tamkar ranta zai fita .

Da gudu Ummu ta nufe Beener tana Rungume ta tare da Fashewa da kuka , Hannu Beenerfa tasa itama tana Rungume Ummu tare da cewa" Ummu dai na kuka , Ai ya tafi ,yanzu kika zo?. Hawaye ne yake bin kuncin Ummu , Hannun ta takama tana cewa " Don ALLAH Beenerfa ki dawo gida Kinji? Idan ba haka ba Kullum Auwalu dukan ki zai tayi . Kema haka yake miki? Beener ta tambaye ta tana shafa gyefen kuncin ta da ya kumbura ga Shatin mari ta ko ina . Cike da damuwa Umma ta amshe su da cewa " ai Ummu tasha dukan shi babu adadi ,mugu marar hali . Eyya Umma kiyi Haƙuri addu'a zaki na masa ba wannan maganan ba.  Beener ce tayi wannan maganan kamin ta kalli Ummu tana sakin murmushi na farin cikin ganin ta .. keda Waye kuka zo?. Cikin kuka Ummu tace " Yah Nurein ."

Yana ina ne bai shigo ba to?. Bari na saka hijab Muje a Shigo dashi . Juyawa Beenerfa tayi tana ɗaukar hijabi a wayar shanya kamin ta saka tana cewa " Muje to .

Tun daga nesa Nurein ya tsaya yana mmkin yau Beenerfa ce da hijab ? Abun da bai taɓa gani ba . Saurin ƙarikawa yayi gaban su yana ware mata hannu alamun tayi hugg ɗin shi ,amma sai ta tsaya tana ɗago idanun ta tare da masa murmushi . Shafin Mari ya Gani kwance a Fuskar ta ,wanda cikin sauri ya sa hannun sa yana tallabo fuskar ta " Beener waye ya maree ki haka?

Wani karen ne???. Yayi maganan cikin doka tsawa .

Hawayen da take danne su ne suka fara ƙwaranya mata , Auwalu ne ,amma laifi nayi masa ban gama girki da wuri ba . Ina yake??. Yayi maganan yana rabata da jikin sa . Saurin riko sa Beenerfa tayi cikin kuka tace " Idan kaje to nima zan tafi ,bazan kuma bari haɗu da kai ba , ka bar shi kawai nace laifi nayi masa . Tsayawa Yayi yana maida huci mai zafi ,zuciyar sa kaman ana watsa masa barkono . Yah Nurein Kayi hakuri muje Umma na jirar mu . Ummu tace tana kama hannun Nurein , danne zuciyar sa yayi kamin yace " Ku muje to".

**

Hankalin Momy da su Daddy Yayi matuƙar tashi ganin babu Ummu a cikin gidan ,sai daga bisani suke jin suna tare da Nurein sun taho Gombe . Zuciya irin a Omar magana ya kasa tun da yaji haka ba magana sai dai da ganin sa kasan komai yana iya aikatawa . Wannan yasa Mom Salma kirar Nurein tare da shaida masa su dawo a yau yau ba sai gobe ba.

